**Sashen APA na International Psychology: Takaitaccen Bayani** **

daga Fatima Yusuf Tumsu

A ranar 21 ga watan Fabrairu , 1997, shugabannin kungiyar Psychology ta Amurka ta amince da sabon sashi na **52** ,“International Psychology,” bayan ɗaukan shekaru ana tsarawa. Manufarta ita ce " ƙara bunkasa da ci gabar dangantakar ƙasa da ƙasa tsakanin masana ilimin halayyar ɗan adam a ɓangaren watsa ilimi , ƙarfafa ziyara, ƙarfafa bincike tsakanin al'adu da kuma haɓaka gudanar da ayyukan asibiti da manufar APA gaba ɗaya . ”

A cikin shekaru 25 na farko, 52 ya tabbatar da sashen rarrabuwar da ba’a cika gani ba tsakanin APA a hanyoyi masu yawa. (1) Yana wallafa manyan karin bayanai na *International Psychology Bulletin,* tare da labaran sakonnin gama gari na asali akan ilimin halayyan ɗan adam a duniya, waɗanda manyan masana ilimin halayyar ɗan adam suka rubuta, ɗalibai da sauransu. 52 kuma ya kaddamar da jarida a cikin shekaran 2011, *International Perspectives in Psychology: Research, Practice, & Consultation*. (2) Ya kirkiri listserv da gidan yanar gizo, yanzu a www.div52.net tare da cikakkun bayanan membobi na yau da kullun. (3) Na gudanar da shiri mai inganci a taron APA na kowane watan Agusta, inda membobin da wanin su za su gabatar da ayyukansu. Shirin APA na farko a cikin 1998 ya ƙunshi masu gabatarwa 120 daga ƙasashe 39. (4) Yana karbar lambobin yabo shekara-shekara na ƙwararru: masanin ilimin halayyar ɗan adam na duniya, masu ba da shawara, bincike na ɗalibi, bincike kan mata/jinsi, fitaccen jerin littattafi, ECP. (5) Yana ba wa membobin sa daman shiga cikin mahimman ayyuka, sabbin jerin littattafan ƙasa da ƙasa tare na wallafan IAP, cibiyar sadarwa mai magana , da rangwame kan littattafai ko wasu kayayyakin.

Tun a farko, 52 ya ji daɗin goyon bayan jagororin APA, gami da Babban Jami'in Gudanarwa Raymond ,D. Fowler. Huɗu daga cikin shugabannin guda 12 na farkon 52 sune shugabannin APA gaba ɗaya: Florence Denmark, Frank Farley, Charles Spielberger, Norman Abeles. Wannan Sashen yana aiki kafaɗa da kafaɗa tare da Kwamitin APA na International Relations a Psychology (CIRP), wanda aka ƙafa a 1944, ta ba da dama wa masana ilimin halayyar ɗan adam da ɗalibai daga Amurka da ma duniya baki ɗaya su shigo Sashen Ƙasa Da Ƙasa na Duniya da kuma damar yin aiki kan ƙaramin kuɗi na shekara-shekara.

A bikin cikar shekara 20th a 2017, shugabannin 52 sun ɗauki sabon tsari mai ƙarfi, domin ci gaba da aikindomin kawo ingattacciyar alaka da sanin ya kamata sakanin ƙasa da ƙasa kan binciken halayyan ɗan adam, ilimi da kuma amfani da shi. Domin samun wasu bayanai, duba gidan yanar gizon 52 , www.div52.net

A yau 52 ta fito matsayin ɗaya daga cikin akƙalla ƙungiyoyin ƙasa da ƙasa guda biyar, kowanne yana da nasa manufa na musamman:

2.IAAP (an kirkira a 1920) ƙungiya ne na International Association of Applied Psychology. A halin yanzu yana da mambobi 2,000 a duk duniya, kuma na taka rawar gani a kwatar mujallar ( (*Applied Psychology: An International Review*), and a quadrennial congress. (www.iaapsy.org).

3. ICP (1941) ita ce International Council of Psychologists. A halin yanzu yana da mambobi 800 a duk duniya, na kuma na taka rawar gani a kwatar mujallar (*International Psychologist* ), da kuma cikin babban taron shekara-shekara. (www.icppsych.tripod.com ).

4. IACCP (1972) ita International Association for Cross-Cultural Psychology. A halin yanzu yana da mambobi 800, yana kuma na taka rawar gani a *Jaridar Cross-Cultural Psychology sau biyu a wata* , da kuma gudanar da taro sau biyu a shekara-shekara. ( www.iacp.org ).

5.IUPsyS (1951) ita ce International Union of Psychological Sciences. Ƙungiya ce mai membobin ƙasashe 75 (babu memba mai zaman kansa), na wallafa jaridan *Journal of Psychology* da kuma gudanar da taron International Congress of Psychology sau huɗu a shekara. (www.iupsys.org).